HA



# Yara da suke neman kariyar kasa da kasa

Bayani akan yara da ba rako ba masu neman damar samin kariyar kasa da kasa a bisa yankin doka na 4 na Dokar (EU) No 604/2013

Mun baka wannan takardar takaitaccen bayani ne saboda ka bayyana bukatar kariya kuma ka samar damu cewa shekarunka suna kasa da 18 ne. Idan kai dan shekaru kasa da 18 ne, za a dauke a matsayin yaro. Za kuma ka ji cewa hukumomin su na kiran ka 'karami' wanda ke nufin yaro. 'Hukumomin' su ne mutanen da ke da hakkin yanke shawara akan ikirarinka na neman kariya.

**Idan ka nema kariya a nan saboda kana tsoro a kasarka ta asali, muna kiran wannan da suna 'neman makafa'. Makafa wani wuri ne na samar da kariya da tsira.**

Idan ka gabatar da bukatarka ta neman makafa zuwa ga hukumomin, doka tana kiran wannan da suna 'neman dama ko bukatar kariyar kasa da kasa'. Mutumin da ke neman kariya ana kiransa 'mai neman dama' Wani lokaci kuma za ka ji mutane suna kiranka 'mai neman makafa'.

Ya kamata mahaifanka suna tare da kai, amma idan ba su nan ko kuma an raba ka da su a hanya, ka kasance **'karamin da ba a rakoba'**.

A wannan yanayi, za mu samar maka da 'wakili', wanda yake babba wanda zai taimaka maka a yayin wannan tsarin. Ita ko shi zai taimaka akan neman damarka kuma za ta/zai iya raka ka idan akwai bukatar kayi magana da hukumomin. Za ka iya tattaunawa tare da wakilinka game da matsalolinka. Wakilinka na nan domin tabbatar da cewa muhimman burinka sune abubuwan farko na dubawa, wannan yana nufin cewa za a duba bukatunka, tsira, lafiya, nishadi da kuma ra'ayoyinka. Wakilinka zai kuma duba yiwuwar sake hadewa da yan'uwa**.**

**Wannan takardar takaitaccen bayanai tana ba da bayani ne kawai. Burinta shine samar da muhimman bayanai ga masu neman kariyar kasa da kasa a tsarin Dublin. Ba ta kirkira/ kumshi dama ba da kanta ko doka Damar da Hakkoki na Kasashe da mutane a tsarin Dublin suna a Dokar (EU) 604/2013.**

**©European Union 2014**
**An amince sake bugawa. Dole ne a nema samin dama daga masu ikon bayar da dama domin anfani ko sake buga hoton wani mutum**




*Wadannan kasashen Dublin sun hada kasashe 28 na Hadin kan Turai (Austria (AT), Belgium (BE), Bulgaria (BG), Croatia (HR), Cyprus (CY), Czech Republic (CZ), Denmark (DK), Estonia (ET), Finland (FI), France (FR), Germany (DE), Greece (EL), Hungary (HU), Ireland (IE), Italy (IT), Latvia (LV), Lithuania (LT), Luxembourg (LU), Malta (MT), Netherlands (NL), Poland (PL), Portugal (PT), Romania (RO), Slovakia (SK), Slovenia (SI), Spain (ES), Sweden (SE), United Kingdom (UK)) har da kasashe hudu "masu alaka" da Dokar Dublin (Norway (NO), Iceland (IS), Switzerland (CH) da Liechtenstein (LI)).*



©European Union

## IDAN AKWAI WANI ABU DA BA KA FAHIMTA BA, TAMABAYA WAKILINKA KO HUKUMOMINMU DOMIN SU TAIMAKA MAKA!

Ko da yake ka nema makafa a wannan kasa, za ta iya kasacewa wata kasa ce za ta bincika bukatar neman kariyarka.

Kasa daya ce kawai za ta iya kasancewa da hakkin kula da bukatar neman kariyaka. An kirkira wannan a wata doka mai suna **'Dokar Dublin'**. Wanna dokar ta bukace mu da mu gano ko mu ne ke da hakkin bincika da takardar neman damarka ko kuma wata kasa ce ke da hakkin – muna kiran wannan 'Tsarin Dublin'.

Ana anfani da wanna doka ne a gabadaya yankin da ya kunshi kasashe 32[1]. Muna kiran wadannan kasashe 32 da suna 'kasashen Dublin' a wannan takardar takaitaccen bayani.

Kada ka gudu daga hukumomin ko zuwa wata kasar Dublin. Wasu mutane za su iya fada maka cewa wannan shine abin da yafi dacewa. Idan wani ya fada maka cewa ka gudu, ko kuma ka bisu tare, ka fada wakilinka ko hukumomin kasar ba tare da bata lokaciba.

Don Allah ka fada ma hukumomin kasar ba tare da bata lokaciba idan**:**

- *Kana kai kadai, kuma kana tunanin cewa mahaifiyarka, mahaifinka, danuwanka ko yaruwarka, goggo[2], kawu[3], kaka mace ko namiji na iya kasancewa a daya daga cikin kasashe 32 na Dublin da ke akan taswirar da ke shafi na 3;*
- *Idan haka ya kasance ko kana so ko baka so ka zauna tare da su;*
- *Ka zo wannan kasa tare da wani kuma, idan haka ne,wanene;*
- *Ka taba zuwa daya daga cikin 'kasashen Dublin' 32 da ke jere;*
- *An dauka hoton zanen yatsunka a wata kasar Dublin: Zanen yatsu wasu zane ne da ake dauka daga yatsunka domin gane ka;*
- *Ka riga ka nema damar samin makafa a wata kasa ta Dublin ta daban.*

## YANA DA MATUKAR MUHIMMANCI KA HADA KAI DA HUKUMOMIN KASAR KUMA KA FADA MASU GASKIYA A KODAYAUSHE.

Shirin Dublin din na iya taimaka maka ida babu mahaifi/mahaifiya da suka rako ka a lokacin da ka nema kariya.

Idan muna da isashen bayani game da su, za mu nema mahaifanka ko yan'uwanka da ke a kasashen Dublin. Idan mun gano su, za mu yi kakari nu hada ku tare a kasar da mahaifanka ko yan'uwanka suke zaune. Waccar kasar za ta kasance mai hakkin bincika bukatar neman kariyarka.

---

**1) Kana da taswirar wannan yanki a shafi na 3.**
**2) Kanwar mahaifiyarka ko kanwar mahaifinka**
**3) Kanin mahaifiyarka ko kanin mahaifinka**

Idan kai kadaine kuma babu wani dan'uwa ko dangi a wata kasar Dublin, akwai matukar tsammani cewa a wannan kasar za a bincika takardar neman damarka.

Za kuma mu iya zabar bincika neman damarka a wannan kasa, ko da ya kasance hakkin na wata kasa ne. Za mu iya yin hakane domin dalilai na taimako, iyali ko al'ada.

Yayin wannan tsari, **za mu kasance masu kula da ra'ayinka**, kuma ba za mu aika ka zuwa wata kasa da muka sani cewa za a take maka hakkinka.

Menene ake nufi da za mu kasance masu kula **da muhimman ra'yinka a kodayaushe**? Yana nufin cewa sai mun:

- bincika ko zai yiwu mu hada ka tare iyalinka a kasa daya;
- tabbatar da cewa kana da tsaro da tsira da kuma lafiya daga mutanen da suke so su maka mugun abu/cutar da kai;
- tabbatar da cewa za ka girma a cikin tsira da hanyar lafiya, da kuma cewa kana da abinci da mahalli da kuma cewa ka sama biyan bukatun nishadinka;
- Kulawa da ra'ayinka – misali, a game da ko kana so ka zauna tare da wani dangi ko baka son haka.




©European Union

## Shakarunka

Mutanaen da suka haura shekaru 18 “manyane” Ana kulawa da su daban da yarda ake kulawa da kananan yara da matasa (“kanana”)

Ka fada gaskiya game da shekarunka.

Idan kana da wata takarda da ke bayyana shekarunka, ka rabata ga hukumomin. Idan hukumomin suka ki aminta da shekarunka, zai yiwu wani likita zai bincika ka domin ya tabbatar cewa kana kasa ko sama da shekaru 18. Dole ne kai da wakilinka ku fara amincewa a tsakaninku game da wannan kafin likita ya bincika ka.

ZA MU YI KOKARI MU ANSA TAMBAYOYIN DA ZA KA IYA FUSKANTA KAMAR YADDA AKA SABA A TSARIN DUBLIN A LAYIKA MASU ZUWA, YADDA ZAI IYA TAIMAKA MAKA DA KUMA ABIN DA ZA KA YI TSAMMANI YA FARU:

## Zanen yatsu – Menene su? Saboda me ake daukar su?

Idan ka bukaci makafa, idan ka kasance dan shekaru 14 ko fiye da haka, za a dauki wani hoton zanen yatsunka (da ake kira "zanen yatsu") kuma a aika da shi zuwa ma'adanar zanen yatsu mai suna "Eurodac". Dole ne ka bayar da hadin kai a wannan tsari – doka ta tilasta a dauki hoton zanen yatsun duk mutanen da suke neman makafa.

Za a iya bincika zanen yatsun ka a wani mataki domin sanin ko ka taba neman makafa a da ko don sani ko an taba daukar hoton zanen yatsunka a wata boda. Idan aka gano cewa ka riga ka nema makafa a wata kasar Dublin, za a iya aika ka zuwa wannan kasar idan kana matukar ra'ayin zuwa can. Wannan kasar za ta kasan mai hakkin bincika takardarka ta neman kariyar kasa da kasa.

Za a adana zanen yatsunka na tsawon shekaru 10. Bayan shekaru 10, za a share su daga ma'adanar bayanan ta otomatik. Idan ka yi nasara kan bukatarka ta neman kariya, zanen yatsunka zasu kasance a cikin ma'adanar bayanan har sai an share su ta otomatik. Idan, daga baya, ka kasance dan kasar Dublin, za a share zanen yatsunka. Zanen yatsunka da jinsinka ne kawai za a adana a Eurodac – ba za a aika ko adana sunanka, hoto, ranar haihuwa da kasarka a maa'adanar bayanaiba. Kodayake, za a iya adana wadanna cikakkun bayanai a ma'adanar kasa. Ba za a raba bayanan da aka adana a Eurodac tare da wata kasa ko kugiya da ba ta kasashen Dublin ba.

Daga ranar 20 July 2015, hukumomi kamar yansanda da kuma ofishin yansanda Hadinkan Turai za su iya bincika zanen yatsunka da kuma bukatar iso ga ma'adanar bayanai ta Eurodac domin kariya, ganowa da kuma binciken manyan miyagun aiyuka da ta'addanci.





©European Union

## Wane bayani ne ya kamata ka tabbatar cewa hukumomin kasar sun sani game da halin da kake ciki?

Akwai yiwuwar za a yi maka tambayi (tambayoyin kanka) domin gano wace kasa ce ke da hakkin bincika bukatarka ta neman makafa. A wajen wadannan tambayoyi, hukumominmu za su yi maka bayanin 'tsarin Dublin' ku za su yi kokarin ganowa idan zai yiwu su hada ka da yan'uwanka da ke a wata kasar Dublin.

Idan kasan cewa akwai mahaifanka, yan'uwanka ko danginka a wata kasar Dublin, kada ka manta ka sanar da mutumin da ke yi maka tambayoyi game da wannan. Samar da isashen bayani kamar yarda yakamata domin taimaka mana gano yan'uwanka – sunaye, adireshi, lambar waya, da suransu.

Yayin tambayoyin, za a iya tambayar ka ko ka taba kasancewa a wata kasar Dublin ta daban. Don Allah ka fadi gaskiya.

Wakilinka zai iya raka ka zuwa wurin tambayoyin, domin taimaka maka da goyon bayanka da yi maka abin da ayafi kamata. Idan kana da wani dalili da ya ba ka so wakilinka ya kasance tare da kai, sai ka gaya wa humomin kasar.

**A FARKON TAMBAYOYIN, MAI TAMBAYA DA WAKILINKA ZA SU YI MAKA BAYANIN TSARIN DA KUMA DAMAR DA KAKE DA ITA. IF AKWAI WANI ABU DA BAKA FAHIMTA BA, KO KANA DA WASU TAMBAYOYI, DON ALLAH KA TAMBAYA!**

Tambayoyi damarka ce kuma tana daga cikin muhimman fanni na neman damarka.

Za a yi maka tambayoyin ne a harshen da ka fahimta. Idan ba ka fahinta harshen da ake anfani da shi ba, za ka iya bukatar mai fassara ya taimaka maka. Mai fassaran zai fassara abin da kai da mai tambaya kuke fadi ne kawai. Tafuntan ba zai kara nashi ko nata ra'ayuka ba. Idan ba ka fahimta mai fassarar ba dole ne ka fada mana da/ ko kayi magana da wakilinka.

Za sirranta tambayoyin. Wannan na nufin cewa babu wani bayani da za ka bayar, tare da cewa ka nema kariya a kasarmu, da za a tura zuwa wasu mutane ko hukumomin da za su iya cutar da kai ko ta wace hanya ko cutar da wani daga cikin yan'uwanka wadanda suke a kasarka ta asalin har yanzu.

**YANA DA MUHIMMANCI YA KASANCE CEWA WAKINKA YA SAN TSAWON LOKACIN TSARIN DUBLIN!**

## Wane tsawon lokaci zai dauka kafin ka sani cewa ko za ka ka tafi zuwa wata kasa ko kuma za ka kasance a nan?

## Menene zi faru idan aka gano cewa wata kasa ce ke hakkin bincika takardar neman damarka?

→ *Idan wannan shine neman makafarka na farko a wata kasar Dublin, za a aika ka zuwa wata kasa saboda mahaifiyarka, mahaifinka, dan'uwa, yar'uwa, goggo, kawu, kaka namiji ko kaka mace na zaune waccar kasar kuma za ka hade dashi/ita/su a can ku zauna tare domin bincika takardar naman makafarka.*[4)]

→ *Idan ba ka nema makafa a nan ba amma ka nema makafa a wata kasa wata kasa ta Dublin a baya, za a iya aika ka zuwa waccar kasa domin hukumomin can su kula da takardar neman makafarka.*[5)]

**A cikin al'amura guda biyun, za iya daukar watanni biyar kafin a yanke shawarar mayar da kai wata kasa, ko daga lokacin da ka nema makafa ko kuma daga lokacin da muka fahinta cewa ka nema kariyar kasa da kasa a wata kasar Dublin. Hukumar za ta sanar da kai game da wannan hukumci da zarar an yanke hukumcin ba tare da bata lokaci ba.**

→ *Idan ba ka nema makafa ba a wannan kasa kuma kuma anki amincewa da takardar neman makafarka a wata kasa bayan anbincika ta, kilan mu bukaci waccar kasa ta mayar da kai, ko kuma mu cigaba da shirin mayar da kai zuwa kasarka ta asali ko inda kake da takardar zaman kasa ko wata kasa uku mai tsira.*

Idan mu ka shawarta cewa wata kasa ce ke da hakkin bincika takardar neman makafarka, yayin da kasar da aka bukata da daukar hakkin bukatun

4) Za ka iya jin mutane suna kiran wanna da suna 'dauki mataki'
5) Za ka iya jin mutane suna kiran wanna da suna 'dauki baya'.

ta aminta da haka, za a sanar da kai cewa ba za mu bincika bukatarka ta neman kariyar kasa da kasa ba amma za mu mayar dakai zuwa kasar da ke da hakkin.

Mayar da kai zai dauki watanni shida daga lokacin da wata ta aminta daukar nauyinka, ko kuma akan hukumcin karshe na daukaka kara ko sake dubawa, idan ba ka yarda da haka ba kuma kana so ka yi korafi akan wannan hukumci (duba sashen kasa wand ke bayanin abin da wannan ke nufi!). Za a iya kara wannan lokacin zuwa shekara daya idan kana gidan kaso, ko watanni 18 idan ka tsere ko gudu



©iStockphoto / Joe Gough

## Menene zai faru idan ba ka son zuwa wata kasa?

### FADA MA WAKILINKA GAME DA WANNAN!

Idan muka yi shawarar cewa za ka tafi wata kasa domin bincika takarda neman damarka a can kuma kai ba ka aminta da haka ba, kana da damar ka yi korafi akan hukumci mayarwan. Muna kiran wannan 'daukaka kara' ko 'sake dubawa'.

Idan ka karba hukumcin mayrwan daga hukumomin, kana da kwanaki 21 domin daukaka kara a Kotun Gudanarwar. Yana da muhimmanci ka bayar da korafin daukaka kara a tsakanin wannan lokacin. Wakilinka zai iya taimaka maka da wanna.

- Kana da kwanaki 7 domin bukatar cewa a dakatar da shirin mayar da kai yayin da ake bincika daukaka kararka. Wata kotu ko majalisar masu shari'a za ta yanke hukumci akan wannan bukata a cikin takaitaccen lokaci. Idan ta hana ka janyewar, za a baka dalilin haka.
- Bayan wannan takardar ya kumshi bayanai game da hukumar da za ka tuntuba domin daukaka karar wani hukumci a wannan kasar.

Yayin tsarin 'daukaka karar' za a baka damar samun taimakon wakilin sharia da, idan ana bukata, taimakon mai fassara da wani tafunta. Za ka iya bukatar taimakon wakilin shari'a a kyauta idan ba ka da kudin biya. Bayan wannan takarda na kumshe da bayanan kungiyoyi da suke bayar da yaimakon shari'a kuma suna iya taimaka maka da daukaka kara.

## Tsarewa

Mutane da ba su da ikon balaguro zuwa inda su ke so kuma suna kulle a cikin wani gida da ba za su iya bari ba sune suke a 'tsarewa'

Idan kai karamin da ba a rako bane za ka iya kasancewa a zaune a wani gida mai dokoki domin ka kasance a ciki da dare ko idan waje yayi duhu ko dokokin da ke nufin sai ka gaya ma mutanen da ke kula da kai idan za ka fita da lokacin da za ka dawo. Wadannan dokoki suna kare tsaronka ne. Wanna baya nufin cewa kana a wurin tsarewa.

### KUSAN BA A TABA TSARE YARA!

**Shin kana a tsare! Idan ba ka sani ba ko a tsare kake ka tambaya hukumomin, wakilanka ko masu baka shawara kan shari'a[6] nan take. Sannan za ka iya yi masu magana game da halin da kake ciki da kuma idan kana a tsare game da yiwuwar yin korafi akan hukumcin tarewar.**

Akwai hadari cewa za ka iya samin kanka a tsare yayin tsarin Dublin. Mafi yawancin lokzci wannan yana faruwa ne idan hukumomin basu yarda cewa kai dan kasa da shekaru 18 bane kuma suna tsoron cewa za ka iya guduwa ko buya daga garesu saboda kana tsoro za a iya aika da kai wata kasa.

Kana da damar a sanar da kai a rubuce dalilin da ya sa aka tsare ka, da kuma yadda za ka iya korafi akan hukumcin tsarewar. Kana kuma da damar taimakon wakilin shari'a idan kana so ka yi korafi akan hukumcin tsarewar, don haka kayi magana da wakilinka ko mai shri'arka idan ba ka ji dadiba.

Idan an tsare yayin tsarin Dublin, tsawon lokacin tsarin za kasance kamar haka: za mu bukaci wata kasa ta dauki nauyin hakkin kula da kai tsakani

---

6) **Mutumin da hukumar ta sani a zaman wakilinka a gurin shari'a. Wakilinka da /ko hukumomin za su baka shawara game da idan kana bukatar daya, amma za ka iya basu dama su samar maka da daya a maimakonka. Duba bayan wannan takardar domin samin kungiyoyi da za su iya baka wakilcin shari'a.**

wata **daya** na bayar da takardarka ta neman makafa. Kasar da aka bukata za ta bayar da martani tsakanin **sati biyu** bayan wannan A karshe, idan ka kasance a tsare, mayar da kai zai kasance tsakanin **sati shida** baya kasar da aka bukata ta aminta da bukatar,

Idan kana so kayi korafi akan mayar da kai din yayin da kake a tsare, hukumomin basu da iko da za su mayar da kai a tsakani sati shida. Hukumomin za su sanar da kai zabukanka.

Idan hukumomin ba su bi dokar lokacin da ya kamata na bukatar wata kasa daukin hakkin kula da kaiba, ko kuma ba su mayar da kai a cikin lokaci ba, za a dakatar da tsaronka a karkashin Dokar Dublin. A wannan hali, za a yi anfani da gayyadadden lokaci da aka saba da ke shafi 11.



©European Union




©European Union

## Menene damarka a lokacin da muka yi shawarar wanene ke da hakkin kula da kai?

Kana da damar kasancewa a wannan kasa idan mu ne ke da hakkin kula da bukatar neman makafarka, ko, wata kasa ce ke da hakin, har sai an mayar da kai can. Idan kasar da kake ciki yanzu ce ke da hakkin bincika bukatar neman makafarka, kana da damar ka saura a nan har sai an yanke hukumcin farko aka takardar neman damar samin makafarka. Kana kma da damar cin anfanin abubuwa, misali muhalli, abinci sa sauran su, haka kuma da kula da lafiya da taimakon kula da lafiya na gaggawa. Kana da damar zuwa makaranta

Za a baka damar bamu bayanai game da halin da kake ciki da kuma kasancewar yan'uwanka a kasar Dublin a bayyane/ko a rubuce kuma, yayin yin haka, kana iya yin anfani da harshenka na asali ko wani harshe da fahimta sosai (ko ka sama mai fassara, idan kana bukata) Za kuma ka karba kwafi na hukumcin mayar da kai zuwa wata kasa. Kana kuma da damar da za ka tuntube mu domin karin bayani da/ko ka tuntuba ofishin Komishinan Kana kuma da damar da za ka tuntube mu domin karin bayani da/ko ka tuntuba ofishin Komishinan Yan gudun Hijira na Majalisar Dinkin Duniya (UNHCR) a wannan kasar.

**Wakilinka da hukumomin kasar za su kara maka cikakken bayani game da damarka!**

## Menene zai faru da bayanan kanka da ka bayar? Yaya ka sani cewa ba za ayi anfani da shi ta wata hanyar da bata daceba?

Hukumomin kasashen Dublin za su iya sauya bayanan da ka basu yayin tsarin Dublin domin cika aikinsu a karkashin Dokar Dublin ne kawai.

Za ka sama damar iso ga:

- Bayanan da suka shafeka Kana da damar ka bukata cewa a canja wannan bayani idan ba daidai bane ko ba gaskiya bane, ko a share idan ba a hada shi ta hanyar bin doka ba.
- Zuwa ga bayanin da ke bayani akan yadda za a bukaci cewa a gyara bayani ko a share, tare da cikakken baynin abokin ma'amala na wasu kayyadaddun hukumomi wadanda aka sani da hakkin tsarin Dublin dinka, da kuma na hukumomin kare bayanan kasa da suke da hakkin saurarон bukatu game da kariyar bayanan kai.

## Ina za ka iya zuwa neman taimako

**Cikakkun bayanan abokan ma'amala na hukuma samin makafa**
Maahanmuuttovirasto (Hukumar Kula da Shige da Ficen Finish)
PL 18, 00581 Helsinki
+ 358 295 419 600
Lambar sabis na wannan sha'ani:
+ 358 295 419 627,
Talata–Alhmis 10–11
www.migri.fi

**Wakilin karami da ba a rako ba**
Kotun gundumar za ta samar da wakili ga karami da ba a rako ba da ke neman makafa. Cibiyar karbar baki za ta bayar da takardar neman dama ga kotun gundumar a madadin wani wakili.

**Kariyar yaro/yarinya**
Ana bukatar cibiyar karbar baki ta shirya duk wasu bukatun jin dadin rayuwa da ake bukata domin lafiyar yaron/yarinyar da kuma bunkasawa daga ma'aikacin da aka wakilta ma shari'ar Idan kana da wasu tambayoyi, yi magana da ma'aikacin jin dadin rayuwa a cibiyar karbar bakinka.

**Hukumar da ke da hakkin tsarin Dulin**
Hukumar Kula da Shige da Ficen Finish (Maahanmuuttovirasto)

Cikakkun bayanan abokan ma'amala da aka fera a sama:

**Cikakkun Bayanan Abokan Ma'amala na Hukumar Lura ta Kasa the (Kariyar Bayanai)**
Tietosuojavaltuutetun toimisto (Ofishin Kariyar Bayanai)
PL 800, 00521 Helsinki
+ 358 295 666 700
Kula da bayanai:
+358 295 616 670,
Litini–Alhmis 9–11 da 13–15,
Jumah 9–12
tietosuoja@om.fi
www.tietosuoja.fi

**Gano mai kula da Eurodac da wakili/wakiliyarsa**
Mazauni: Rundunar Yan Sandan ta Kasa (Poliisihallitus) da Hukumar Kula da Shige da Ficen Finish (Maahanmuuttovirasto)

**Cikakkun bayanai na ofishin mai kula**
+ 358 295 480 181
Poliisihallitus (Rundunar Yan Sandan ta Kasa)
PL 22, 00521 Helsinki
kirjaamo.poliisihallitus@poliisi.fi

Maahanmuuttovirasto (Hukumar Kula da Shige da Ficen Finish)
PL 18, 00581 Helsinki

+358 295 419 600
Lambar sabis na wannan sha'ani:
+358 295 419 627,
Talata–Alhmis 10–11
www.migri.fi

Idan kana so ka duba bayani da ya shafe ka wanda aka nada a sistem din Eurodac, bayar da wata bukat ofishin yansanda. Ka shiya da nuna wasu shaidu na kanka. Muna ba da shawara ka tuntuba ofishin yan sandan da ya karba takardar neman damar samin makafarka. Akwai bayanan abokan ma'amala na ofishin yansandan a Sashen Yanar Gizo na Yansanda a poliisi.fi.

**Suomen Punainen Risti (Kungiyar Finnish Red Cross)**
Tehtaankatu 1 a
00140 Helsinki
+358 20 701 2000
info@redcross.fi
www.redcross.fi

Bincika batattun yan'uwa.

**Ofishin masu ba da taimakon shari'a da Kungiyoyin goyon bayan yan gudun hijira**
Ana samun taimakon shari'a daga ofishoshin sharia da kuma atoni wadanda suka sanar cibiyar karbar baki game da shirinsu na taimakawa mai neman makafa. Domin karin bayani game da taimakon shari'a, yi magana da ma'aikatan cibiyar karbar baki.

**Cikakkun bayanan Kungiyoyin Kasa da kasa na Barin Kasa (IOM)**
IOM Helsinki
Unioninkatu 13, hawa na uku
PL 851, 00101 Helsinki
+358 9 684 1150
iomhelsinkiavr@iom.int
www.iom.fi

Idan kana so ka koma kasarka ta asali da kanka, nema shawara a cibiyar karbar baki.

**Ofishin Babban Komishinan Yangudun hijira na Majalisar Dinkin Duniya mafi kusa**
UNHCR
Ynglingagatan 14, 6 tr
SE-113 47 Stockholm
Sweden
Tel. +46 8 457 48 80
swest@unhcr.org

1.9.2016 hausa

European Commission

MAAHANMUUTTOVIRASTO
MIGRATIONSVERKET
FINNISH IMMIGRATION SERVICE

POLIISI
POLISEN I FINLAND
Police of Finland

Rajavartiolaitos
Gränsbevakningsväsendet
The Finnish Border Guard